**Vol. 11 No 10**
***September 1999*** ***(Hausa)*** ***CHANGE Radio***

# Ga Abubuwan Dake Ciki


| | Locaci | Shafi |
|---|---|---|
| **Kudancin Afrika na fuskantar matsalar cutar kanjamau**<br>*Kimanin mutane dubu 50 ke kamuwa da cutar kanjamau a Afrika ta kudu kowani wata.* | 1min. 45secs | 6 |
| **Afrika na fuskantar yunwa**<br>*Yake-yake, kamfar ruwa da kwari suna sayawa abu mawuyaci ga kasashen Afrika wajen ci da kansu* | 1min. 37secs | 3 |
| BUNKASAR ALKARI'U CIKIN HANZARI A AFRIKA<br>**Alkari'un Afrika suna bunkasa cikin hanzarin fiye da sauran kasashen duniya** | 21secs | 13 |
| **Afrika na samawa kanta kasuwa**<br>*Afrika na shirin jayo hankalin masu zuba jari na duniya* | 2min. 45secs | 7 |
| **Gibi Tsakanin Maza da mata kan ilmi a makarantun Afrika**<br>*Yaran maza ke shiga makarntu fiye da mata a yawancin kasashen Afrika* | 46secs | 13 |
| **Sabon Maganin kare jarirai daga cutar kanjamau**<br>*Sabon maganin da aka samu a Uganda da Amurka na bada kwarin gwiwa ga 'yan baya masu zuwa* | 1min. 32secs | 6 |
| **Azabtar da yara ya zama ruwan dare a Uganda**<br>*Yara a kasar Uganda suna fusukantar bakar azaba daga iyayen su* | 2min. 3secs | 10 |
| **Mata da yawa ke zaman jarun a kasar Sudan**<br>*Cinikin barasa ya jefa matan kudancin Sudan dubbai gidan jarun a kowace shekara* | 1min. 53secs | 5 |
| **Bacewar halittu a Duniya**<br>*'Yan baya masu zuwa bazasu gafarta mana ba saboda halakar da wasu halittu da jama'ar yanzu keyi.* | 2min. 45secs | 7 |
| **Za'a gabatar da wani shirin kare kogunan turai**<br>*Hukumar WWF ta shirya kaddamar da yekuwar kare kogunan kasashen turai.* | 1min 11secs | 5 |

| | | |
|---|---|---|
| **Kasar Canada na da muhimmanci kan gandun dazuzzuka a duniya**<br>*Kimanin kashi goma cikin dari na gandun dajin duniya na kasar Canada* | 26secs | 14 |
| **Matsalar karancin ingantacen ruwa**<br>*Kusan kowani mutun guda daga cikin mutane uku a duniya zai fuskanci matsalar karancin ruwa nan da shekaru 50* | 14secs | 13 |
| **Shinkafaa mai yawa da ruwa kalilan**<br>*Rashin isashen ruwan sama a duniya na jefa noman shinkafa cikin mawuyaci hali, masana kimiya na samo sabbin dabarun noma da ruwa kalilan.* | 2min. 34secs | 8 |
| **Zanzibar ta haramta shigo da kifin tabki**<br>*Zargin yin amfani da guba ya sanya an haramta shigo da danyen kifi da ake kamawa daga Tabkin Victoria a gabshin Afrika.* | 1min. 50secs | 4 |
| **Najeriya ta kafa sabbin Gandun Dazuzuka**<br>*Wasu gandu dazuzzuka biyu an maida su na kasa* | 51secs | 3 |
| **Italiya na daukar Tsauraran matakai kan masu cinnawa dazuzzuka wuta**<br>*Italiya ta kuduri aniyar dakatar da masu cinnawa gandun dazuzzuka wuta* | 44secs | 13 |
| **Tauraron dan adan zai iya gano alamar barkewar annobar zazzabi**<br>*Bayanin tauraron dan adan zai taimaka wajen kare mummunar annobar dabbobi.* | 2min. 7secs | 9 |
| **Tsuntsayen dake sanin lokaci**<br>*Masana sun gano abin mamaki a kasar Indonesia* | 59secs | 14 |
| **Zaki da bera**<br>*Aikata alheri* | | 10 |
| **Meyasa jemagu ke tashi da dare?**<br>*Jemagu suna gani da dare* | 1min. 5secs | 11 |
| **Mumunar laifi da kadima kurege ya aikata**<br>*Gano dalinlin da yasa damisa ke farauta ita kadai* | 4min. 10secs | 11 |

# *Labaru*

**Afirika na fuskanta yunwa** **1min. 37secs**

Sama da mutane miliyan goma daga kasashen Afrika goma sha-6 ne ke bukatar taimakon gaggawa na kayan abinci domin kaucewa yunwa. Wanan kuwa na kunshe ne cikin bayanin da hukumar kula da abinci da aikin gona ta duniya dake birnin Roama ta bayar.

Yakin basasa, kamfar ruwa da kwari, sune suka gurgunta aiyukan samar da abinci a sashin Sahara na Afrika, inda dubban daruruwan mutane ke fuskantar barazanar yinwa inji hukumar a ranar 16 ga watan Agusta.

Ance kasar Angola ce barazanar tafi muni, inji jami'in hukumar ta abinci Mrs. Mwita Rukandema, wadda tace kazancewar yaki kwanan nan tsakanin dakarun Gwamnatin Angola dana 'yan twayen kungiyar UNITA, ya sanya baby damar kai duk wani taimakon kayan abinci ga jama'ar da suka gudu suka bar gidajen su a sandiyar fadan.

Dakarun na UNITA, wadanda aka bada rahoton cewar su nayiwa motoci kwanton bauna tare da harba mayan makamai a manyan garuruwan kasar.

Jami'ar Rukandeman tace in har wannan hali ya cigaba man da watani biyu, za a ji mugun labari game da matsananciyar yunwa.

Rukandema tace hanya guda da za'abi domin kaucewa wannan bala'i, itace ta matsawa dakarun Gwamnati dana 'yan tawayen lamba, domin kyale yin amfani da jiragen sama, sauka a wasu filayen jiragen same 'yan kalilan wajen kai kayan abinci da magunguna.

Dayawa daga cikin 'yan kasar ta Angola da baki 'yan kasashen waje da sukayi kokarin kai kayan abinci, 'yan twayen su kashe su.

*Africa News On Line.*

**Nageria ta kafa sabbin gandun dazuzuka** **51secs**

Ranar 3 ga watan Agusta Gwamnanti Najeriya ta kaddamar da gandun dajin Okomu dake kudancin kasar da gandun dajin Kamuku dake arewacin kasar a matsayin gandun dazuzuka na kasa.

An kafa gandun dajin Okomu nee shekaru goma sha-5 da suka wuce dake gandun dajin a matsayin na gwaji, wanda hukumar kula da dazuzuka na Najeriya, wanda ke karkashin hukumar kare dabbobi da halittu ta duniya (WWF). Gandun dajin dake da fadin kilomota dari da goma sha-2 murabba'I, wuri ne dake da dausayi da tsuntsaye iri-iri dakuma namun daji iri-iri ciki har da giwaye dakuma birra masu farin wuya.

Wanan kuwa gagarumin ci gaba ne da aka samu inji darektan kula da gandun dazuzika na kasa, Alhaji Lawan Marguba.

*Paddy Ezeala/WWF*

**Zanzibar ta haramta su a tabki** **1min 50 secs**

Kasar Zanzibar ta harmta shigo da kifin da aka kama daga Tabkin Victoria, watanni biyu bayan kungiyar kasashen Turai ita ma ta haramta shigo da irin wadan nan kifin daga yankin, a sakamakon rahotanin da aka bayar na cewar masintan yankin na amfani da guba wajen kamun kifin.

Cikin sanarwar da Ministan gona da, raya dabbobi da albarkatun kasa, tace anyi haka ne domin kare masu cin kifin ciki harda masu zuwa yawon bude ido dakuma tattalin arzikin tsibirin.

Burgediya-Janar Adam Nwakanjuki yace koda shike babu tabbas kan ko tabkin na Victoria ya gurbace da guba, kasar Zanzibar ba zata yi kasadar kasancewa wurin da za a rika jigbe kayan abincin da suka lalace ba.

Haramcin wanda ya hada da kifin da aka samu daga kogin Nilu ya biyo bayan yadda ake kara samun irin wadan nan gurbatatun kifayen daga kogin na Nilu. Yanzu haka Gwamnati ta sanya jamian da zasu rika sa ido a tasoshin jiragen ruwa dake tsibirin dakuma tasoshin jiragen sama da Otel-Otel dakuma manyan kantunan ciniki irin na zamani, danufin hana shigo da kifayen da ake samu daga tabkin na Votoria da kuma kogin na Nilu.

Wani babban jami'in hukumar kula da yawon bude ido na Zanzibar yace duk Otel din da aka samu yan amfani da wadan nan kifin, za a soke lasisin sa. A makon jiya ne Gwamnatin Tsibirin ta umurci dukkan otel-otel din da suke da kifayen na kogin Nilu da su lalatasu.

Haramta sigo da kifaye daga Gudarin kasar Tanzania da Kenya dakuma Uganda yazo ne makwani uku kacal bayan da Zanzibar ta haramta saida wani irin ruwan kwalba da ake kira MASAFI, wanda akeyin sa a Dar es Salam. Gwamnati Tsibirin tayi ikirarin cewar kwajin da aka gudanar daga jamin'an kula da harhada magunguna an gano cewar ruwan bai dace jama'a su sha ba.

*Africa News On Line*

**Shirin kare kogunana turai** **1min 11secs**

Za afara wani gagarunin shirin kare kogunan kakashen Turai daga wannan watan na Satumbar 1999. Shirin wanda akayiwa taken ‘Rayayyun Koguna’ zai kunshi dukkan nhiyar, wada hukumar kare halittu da dabbobi ta duniya WWF zata aiwatar. An tsara shirin ne ta yadda za a wayarwa da jama’a kai su san muhimmanci da aiyukan koguna tare da nuna irin barazanar da suke fuskanta saboda rashin kulawa tare kuma da irin rawar da jama’a da kungiyoyi zasu taka wajen kula da ruwa.

Kamar yadda hukumar ta WWF ta fadi shirin yekuwar zai samarwa da kogunan na Turai da tsarin kula tare da manufofi na kwarai.

Za’a kaddamar yekuwar ne a Brussel ranar 21 ga watan Satumba, a halin yanzu kuma za a kaddamar da wani littafi mai warka 20 a karshen watan Agusta, wanda ke da taken RAYA KOGUNAN TURAI. Tsarin sha yanzu magani yanzu. Shirin na sha yanzu magani yanzu, zai kalubalanci kungiyar kasashen Turai, Gwanmatocin kasashen da kananan hukumoni masana ‘antu da ‘yan kasuwa, masu samar da ruwa da sauran kungiyoyin da ke da sha’awa a wannan fanin, domin daura damara wajen daukar matakan da suka dace, inji hukumar ta WWF.

*WWF*

**Mata da yawa ke zaman jarun a kasar Sudan** **1min 53secs**

Sama da mata dubu talatin ne suke zaman jaron na wa ‘adi dabab-daban a Sahin Arewacin kasar Sudan inda Musulmi ke da rinjaye, akasarin su saboda aikata kananan laifuffuka.

Wannan kuwa yafi kashi daya cikin dari na yawan al’umar kasar. Kashi casa’in da biyar cikin dari na wadan nan matan a daure su ne saboda laifin girka barasa dakuma sayarwa, kuma kusan dukkan su sun fito ne daga sashin kudancin kasar ta Sudan inda ba laifi bane girkawa ko saida barasa dakuma dirkan sa.

Kamar yadda rahotanin baya-bayan nan ya nuna fiye da rabin adadin Matan an sake kama su ne bayan da aka sako su. Kayan da ake girka barasan kuwa wasu matane fittatu ne ke sayar dasu da arba ta hanyar gwanjo inji rahotannin. Matan su kan baron gidan kason ne su je su sayi kayan girka barasan kana su cigaba da sana’ar ta su da suka saba.

Akasarin matan dai masu juna biyu ne ko kuwa suna shayar da jarirai. Fiye da yara dari a ke haihuwar su a kowace shekara a daya daga cikin gidajen jarun din, yayinda wani gidan akan haifi kimanin yara dari biyu yayinda iyayen nasu ke zaman kaso.

Koda shike ance gidajen Jarun na Sudan na daya daga cikin mafiya kyau a Afrika, tuni ake da kira domin sake tsarin gidajen ta yadda za arika kula da matan da suke fama da tasku a sashin Arewacin kasar saboda al'adar su ta saida barasa.

*Newslink Africa*

**Sabon maganin kare jariban da iyayen su ke fama da cutar kanjamau** **1min 32secs**

An samo wani sabon maganin da zai iya kare jariran da iyayen su ke dauke da cutar kanjamau, kamar yadda binciken da wasu masana daga kasashen Amruka da Uganda suka gudanar a Kampala da Washington.

Sakamakon farko da aka bayar baya aiyukan bincike na shekaru biyu ya nuna cewar maganin zai kare jaririn da uwar sa ke dauke da kwayoyin cutar HIV, wanda ke kaiwa ga cutar kanjamau, in har anywa uwa wannan maganin yayinda take haihuwa dakuma shi jarinrin bayan yayi kwana uku da haijuwa.

Ana cin karfin cutar da kimanin rabin karfin ta ta hanyar amfani da wannan sabon maganin, idan aka kwantata da maganin AZT-, wanda ke da tsada ninki 70, kamar yadda ma'aikatar lafiya ta Amurka tayi bayani. Wanan bincike shine mafi muhimmanci da ingaci yazuwa yanzu kan kokarin da akeyi na kare yaduwar wannan muguyar cutar ta kanjamau tsakanin iyaye mata da jariran su a duniya inji Dr. Anthony S. Fauci na tsangayar kula da cututtuka masu yaduwa, wanda ta dauki nauyin tafiyar da binciken.

Haka kuma wannan sakamakon ya samu gagarumin marhabin a Kampala. Wannan bincike ya bada kwarin gwiwar cewar akwai alamun kare jama'ar kasashen Afrika masu zuwa nan gaba daga kamuwa da ita wannan cutar ta kajamau, inji Ministan kula da aiykan lafiya na Uganda Cripus Kiyonga.
Newslink africa

## *Sharhi*

**Kudacin Afrika na fuskantar matsalar cutar kanjamau** **1min 45secs**

Cutar kanjamau ta fara faskara a kudancin Afrika duk da kokarin da Gwamnatoci da kungiyoyi masu zaman kansu da sauran al'umomi keyi na wayarwa da jama'a kai game da matsalar cutar.

Daga kididdigar da aka gudanar ta nuna cewar kasashen Botsuwan, da Namibia da Swizaland dakuma Zimbabwe sune cutar tafi muni a kudancin na Afrika. Kusan rubuin al'umar kasashen duk sunharbu da kwayoyin cutar ta HIV ko kuwa cutar kanjamau din baki daya. Kusan rubu'in wadanda suka kamun, mutane ne da shekarun su ya kama daga goma sha-5 zuwa arba'in da tara.

Kamar yadda Mujallar TIME ta Amurka ta wallafa ma'aikatar lafiya ta Afrika ta Kudu tayi kiyansin cewa, akalla kashi 20 cinkin dari na yawan ma'aikatan kasar ne zasu kamu da kwayoyin cutar yazuwa badi. Cinkin shekaru uku man gaba kuma kimanin mutane dubu metan da hamsin ne za su rika mutuwa a duk shekara a sansadiyar cutar wadda zata bar muatane dubu dari shida marayu. Haka kuma cutar zata rage yawan shkarun da ake saran mutane za suyi da shekaru ashirin hakan zai sanya tattalin arzikin kasar ya rago da kashi biyu cikin dari.

Cutar zatayi matukar illa ga tattalin arziki, muddin ba a bullo da kwararan matakai da shirye-shirye ba wadanda zasu kyautata harkokin kwadago da ingantuwar aiki, kamar yadda rahoton hukumar raya kasa ta duniya UNDP ta bayar.

Ministan lafiya na Afrika ta kudu Nkosazan Zuma yace mutanen kasar suna kamuwa da kwayoyin HIV cikin hanzari, wanda a duk wata kimanin mutane dubu hamsin ne ke kamuwa da cutar. Wanan kuwa baban hatsari ne ga kasar. Hakan ya nuna akwai gyara bisa damarar da kasar tayi na yaki da yaduwar cutar ta kanjamau.
*Newslink Africa*

**Afrika na samun karbuwa kan kasuwanci 2min 45secs**

Ganin demukuradiya ta kankama a Afrika, mayan kasashen duniya sai nuna sha'awa sukeyi game da zuba jari a nahiyar. Cikin watan Oktoba, za'ayi taron kwanaki biyu a Dakar ta kasar Senegal, inda manyan kasashen duniya da kungiyoyin raya kasa zasu hallara domin tattaunawa. Daga cikin wadanda zasu hallara su hada da Ministoci daga kasashen Turai da manyan kamfaonin 'yan kasuwa da sugabanin Afrika da Minintocin su na kudi. Kamar yadda mjallar Newslink Afrika ta ruwaito baki daga kasashen Turai sun hada da Ms. Clare Short Sakatariyar kula da raya kasashe na Biritaniya, da Mr. Paul Neilson Ministan raya kasashe na Denmak. Sauran sun hada da Mr. Kenzo Oshima babban darektan tattalin arziki da raya kasashe dake Japan da Ms. Hilde F. Johnson Ministar raya kasa da kasa da kare hakkin dan adam na Norway.

Haka kuma Ms. Evelyn Kerfkens Ministar raya kasashe ta Netherlands da manyan jami'an kasashen Faransa da Jamus da Finland dakuma Italiya duk zasu halarci taron. Taron na hadin gwiwa ne tsakanin kungiyar raya masan'antu la duniya UNIDO, da kungiyar habaka masan'antu ta Afrika (AAI) da hukumar raya tattalin Arzikin Afrika (ECA) da Bankin raya Afrika (ADB) dakuma kungiyar hada kan kasashen Afrika (OAU).

Daga cikin batutuwan da za a tattauna a taron su hada da tsarin bunkasa masana'antu a Afrika da yanayin harkokin zuba jari a haniyar dakuma hadin ka yankuna da kawancen kungiyar Tuari da Afika da sha'anin samar da kudaden kafa kananan masana'antu.

Taron na Oktoba ya biyo bayan yekuwar Harare ne da akayi a shekarar 1997. Yekuwar ta sanya babban sakataren kungiyar OAU tare da hukumar raya kasa UNIDO da babban sakataren hukumar ECA kan su shirya taro da manyan kasashen dake bada taimako na duniya ta yadda za a samo hanyoyin samar da kudaden aiwatar da aiyukan raya kasa na sha yanzu magani yanzu.

Masu shirya taron suna fatar taron zai gaggauta habaka masana'antu a Afrika ta hanya baiwa kasashen Afrika damar samun sabbin abokan huldar kasauwanci ciki da wajen nahiyar ta Afrika.

Hadin kai ta fuskar fusaha shine babban jigo wajen kyautata yanayi domin zuba jari a kasashen da dama. Haka kuma zai kara kyautata samar da masana'antu masu karfi na 'yan kasa, wadanda zasu tafi tare da manyan masu zuba hannayen jari na kasashen duniya, inji rahoton da Newslink Afrika.

*Newslink Africa*

**Shinkafa mai yawa da ruwa kalilan** **2mins 34secs**

Kokarin gaggawa da akeyi na samar da wata dabarar noman shinkafa tare da ruwa kadan kwalliya ta fara biyan kudin sabulu. Domin kuwa an samo wata dabarar noman shinkafa mai yawa da ruwa kalilan. Kungiyar binciken aikin gona da bayar da shawarin kwaruru ta duniya CGIAR ce ta bullo da dabarar samar da dausayi da ingantacen iri, da kyautata filayo domin noman shinkafar.

Ita wannan sabuwar dabarar ta rage yawan muhimmancin samar da ruwa, domin samun amfani mai yawa kan kowace dadadar gona. Saidai kuma kungiyar ta CGIAR bata bada dalla-dallar bayani kan yadda sabuwar dabarar zatayi aiki ba. Duk da haka shugaban kungiyar Isma'il Seragendin kuma mataimakin shugaban Bankin Duniyan kan aiyuka na musamman yace shinkafa tana bukatar ruwa ninki biyu fiye da kowace tsaba kana sama da tan dubu biyu na ruwa ake amfam\ni dashi domin noma tan guda na shinkafa. Wanan yanayi kuwa zai kasance mawuyaci ganin yadda ake samun koma baya kan samar da ruwa tare da yawan bukatar samun shinkafa a duniya.

Fiye da rabin mutanen duniya zasu dogara ne kan shinkafa, nan da shekaru 30 masu zuwa. Yankunan da ake noma shinkafa a sashin Arewachi da Kudancin Najeriya suna fuskantar baranzanar giggina madatsun ruwa, dakuma bukasar alkari'u watakila sabuwar dabarar ta farfado da nomar shinkafa sannu kan hankali. Ganin yadda ake asarar filayen noma cikin hanzari, domin bunkasar garuruwa da lalacewar dausayin kasar noma matsalar ta zama babba da ake fuskanta inji babban Darktan kungiyar ta CGIAR Ronald Cantrell dake da cibiya a kasar Filifin.

Sabuwar dabarar tana iya taimakawa wajen kyautata tattalin arzikin kasashe masu tosowa na duniya. Akasarin kasashen dake nomar shinkafa kasashe ne masu tasowa wadanda Bankin duniya yace samun su dan kalilan ne. Nahiyar Asia na da kasashe goma sha-7 daga cikin kasashe 25 manya dake noma shinkafa. Suna nome fili mai fadin kashi case'in daga cikin dari na yawan filayen da ake noma shinkafa a duniya suna samar da kashi casa'in cikin dari na shinkafar da ake nomawa a duniya. A hakikan gaskiya ma kashi daya cikin uku na kasashen Asia dake noma shinkafa ce suke nomawa a ciki.

*CGIAR*

**Hango barkewar zazzabi mai Tsanani ta hanyar tauraron-dan adam 2mins 7secs**

Ana iya kare aukuwar barkewar kwayoyin cutar nan dake haddasa cutar dake kashe garkunan shanu masu yawa a gabshin Afrika, wanda kuma ke janyowa jama'a shiga halin tasku. Daga binciken da aka gudanar ya nuna cewar cutar tana da sahihiyar hanyar da take sake zagayowa. Ana iya hango sake zagayowar cutar watani hudu kain aukuwar ta, ta hanyar yin amfani da tauraron dan adam dakuma daukar matakan lalata kwayoyin cutar.

Masu binciken su gano cewar zagayowar cutar a ko yaushe yanayin kicibis da daminar da aka samu ruwan sama mai yawa a yankunan masu yawa na gabashin Afrika. Sunyi nazain yanayi na shekaru hamsin, sun gano cewar, cutar ta bulla shekaru goma sha-7 da suka wuce, wanda kuma yayi kicibis da daminar da aka samu ruwan sama mai yawa. Daga bisani kwayoyin cutar sukan bace tsakanin bullowar ta.

Wanan kuwa cibiyar binciken kimiyar Amurka NASA da ma'aikatar kare kwayoyin cuta ta duniya dake cibiyar bincike ta Walter a Washington DC ne suka gano.

Kamar yadda bincike ya nuna, Sauro Aedes dake yada kwayoyin cutar, suna sanya kwayoyin ne a kwayayen su, wanda duma ke yaduwa a wuraten dake da dausayi bayan da aka samu ambaliyar ruwa. Su kuwa kananan Sauron suna samun abincin su ne a jinkin dabbobi. Haka abin zaiyi yaduwa ba tare da la'akari ba har sai sun yadu sosai. Dabbobin da suka ci wadan nan kwayayen Sauron su zasu kamu da cutar, wanda daga bisa in mutane sunci naman dabbobin sai su rika kamuwa da cutar zazzabin mai tsanan. Shi kuwa irin wannan Sauron yana yaduwa ne a locacin da aka samu damuna mai ruwa sama sosai.

Masu binciken suce wannan tauraron dan adam zai taimaka wajen hango ko hasashen barkewar annobar cutar watani shida kafin aukuwar sa. Abin sha'awar anan shine tauraron dan adam din, zai iya yin gargadi tun kafin barkewar annobar, kana ya gano ainihin yankunan da abin zai faru, inji wani kwararen masanin halittu Compton Tucker, wanda yayi amfani da tauraron dan adam, wajen yin nazarin halittu a Afrika na tsawon shekaru 20.

*Environmental News Network*

**Azabtar da yara ya zama ruwan dare a Uganda** **2min 3secs**

Iyaye suna yawan dukan 'ya 'yan su tare da yi musu fyade ba kuma tare da an dauki matakan shawo kan lamarin ba. Wannan kuwa na kunshe ne cikin rahotton da jaridar Monitor da ake bugawa rana-rana a Uganda ta 13 ga watan Yuli.

Jaridar ta ruwaito cewar wani locain anayiwa yara dukan kawo wuka a gidaje da makarantu. Wasu ma har kashe su akeyi ta hanyar azabtarwa daga su iyayen saboda 'yan laifukan da basu taka kara su karya ba, irin su samartakar Bera ko rashin kawowa uban su agogo cikin lokaci yayinda yake kokarin zuwa aiki. Hanyar da akafi azabtar da yara, itace da daure hannun su da igiya, kana a rufe da ganyen ayaba ko takarda, kana a sanya a kan wuta inji jaridar. Haka kuma jaridar ta Minitor tayi tir kan yadda akeyiwa yaran mata kanana fyade, wasu kan dududu ba su wuce shekaru uku da haihuwa ba.

Kwanan nan ne Gwamnatin Uganda ta daga yawan shekarun yiwa 'yan mata aure daga goma sha-4 zuwa goma sha-8, domin kare su. 'Yan kasar Uganda da abin ya dama suna kura da babbar murya kan Gwamnati ta kara yin kuduri wajen kare yara mata. Babbar mataalar azabtar da yara, shine Gwamnati ba ta dauki batun da muhimmanci ba inji jaridar ta Minitor, cikin sharshi ta. Baya ga kungiyoyi masu zaman kansu, Gwamnati bata kashe kudi wajen gudanar da bincike, ko shirya taruruka na kasa ta yadda za a karfafa gwiwar shawo kan wannan matsala ta azabtar da yara.

*Africa News On Line*

**Zaki da bera**

Zaki wanda ake dauka a matsayin sarkin dawa, saboda karfin da yake dashi yana kuma ladabtar da duk wata dabbar da ta nemi wuce makadi da rawa. Domin haka dukkan mamun dawa suna tsoron sa kuma suna masu biyayya gare shi, bugu da kari kuma suna bakin kakarin su na kaucewa duk wani abu da zai bata masa rai. Dukkan dabbobi suna kokarin ganin dangantakar su da sarkin dawa Zaki ta kara kyautatatuwa.

Wata rana Zaki na barci, sai Bera cikin rashin sani ya taka bancin sa. Yayinda zaki ya tashi cikin fushi, sai ya kama bera yana son ya kashe shi, shine bera ya roki sarkin dawa da yayi masa rai. Yace watakila wata rana shima zai taimakawa zaki. Shine zaki yayi mamaki, har abin ya bashi dariya, ganin bera dan tsurut dashi har yace zai iya taimakawa zaki, wanda shine sarkin dawan dabbobi. Duk da haka dai sai ya sake shi amma fa sai da ya ja kunnen sa kan kada ya kuskura ya sake tadashi daga barci. Bera yayi godiya kana ya tafi gida.

Baia dade ba da yin haka, ran nan sai zaki na yawo cikin daji, sai ya fada cikin tarkon da maharba suka kafa. Yayinda zaki yayi ta ruri, domin neman dauki, dukkan sauran dabbobin sai sukayi biris dashi, tunda yake suna tsoro in har sun sako shi yana iya halaki su. Daga karshe dai sai bera yaji kukan zaki, sai ya tuna da irin alhinin da zaki yayi masa yayinda ya taka hancin sa yana barci, domin haka sai ya kuduri aniyar zuwa ya taimaka masa.

Yayinda ya doso zaki sai ya ga ashe taron na kirtani ne. Sai bera ya fara daddatse kirtanin da hakoran sa kan ajima sai gashi yayi katuwar kofa ta yadda zaki zai iya fita. Yayinda bera ya ceci zakin sai yace dashi, yayinda ka ceci rai na nace dakai nima watalila wata rana zan cece ka, sai kayi dariya, kace sarkin dawa da kanka yaya ni bera zan iya taimaka maka.
Domin haka dai aikata alheri ga kowa, ba asan gobe ba.
*Character moulding Stories for Better Citizenship.*

**Meyasa Jamagu ke tashi da dare 1min 5secs.**
Jamagu kamar sauran dabbobi basu da wata hanyar kare kansu. Domin haka dahun dare shine makarin su. Babban abokin gabar su shine Duji, wanda ke yawo da dare domin neman abinci yayinda suma jemagu ke barin wuraren zaman su irin su kogo ko kuwa bishiyoyi. Wasu daga cikin jemagun suna cin kwari, yayinda ba mai ganin su. Saboda haka jemagu suna yawo ne cikin dare saboda kare kan su, dakuma samun abincin su cikin sauki.

Daga cikin dukkan dabbobin duniya jemage ne dadai ke tashi kamar tsuntsu. Fukafukin su fata ce da ta lullube yatsun su dakuma dogayen kafafun su har baya. Wasu mutanen suna daukar cewar jemagu basa gani. Kokadan ba gaskiya bane Domin kuwa jemagu suna da idanu dana suna gani saari cikin dare.
*Chongololo*

**Mummunan laifin da Kurege Kadima ya aikata 4mins 10secs**
Wata kabila da ke kira Hambakush dake kudancin Afrika, sun bada labarin wani kureje da wata damisa da ‘ya ‘yan ta. Sun kulla yarjejeniyar cewa, kureje zai rika kula da ‘yan ‘yan damisar yayinda ta tafi neman abinci, ita kuwa damisar zata rika baiwa kureje abinda ta samo daga wajen farautar ta. Sunan kureje Kadima ita kuwa damisa suna ta Nthoo.

Ita wannan yarjejeniyar tayi ta aiki tsakanin su, har yazuwa locain da aka samu kamfar ruwa a kasar. Namun dajin da ita Nthoo take farautowa duk su gudu zuwa yankunan dake da ruwa, domin haka damisar ta fara fuskantar mawuyacin hali na rashin abinci tare da Kadema dakuma ‘ya ‘yan ta. Kwanan da kawanki Nthoo yadda ta tafi haka take dawowa hannun ta rabbana babu abinci. Nan da nan yunwa ta fara addabar su.

Wata rana Ntooo ta komo daga wajen faruta sai ta samu Kadima na cin nama, shine sai ta tambayeshi ko ina ya samu abinci, yayinda itama da ta shiga daji domin neman abin kalce bata samu ba. Sai Kadima ye kada baki yace, wata 'yar karamar dabba ce tazo wucewa bakin kogo, shine na kokarta na kashe. Amma gaskiyar lamarin shine naman da Kadima ke ci naman daya daga cikin 'ya 'yan damisar ne.

Washe gari Nthoo ta fita faruta, sai Kadima ya sake kashe daya daga cikin 'ya 'ya ta biyu da suka rage ya cinye. Yayinda damisar ta komo da marice hannun ta rabbana Kurege sarkin wayo, sai ya dauko mata dan nata guda da ya rage, bayan ta bashi nono sai ya shigar dashi ya sake fitowa dashi yace ga na biyu, bayan ta bashi nono sai ya shigar dashi ya sake fitowa dashi yace ga na biyu, bayan ta bashi nono ya sake komawo dashi ya fito dashi yace ga na ukun su.

Washegari bayan da Nthoo ta fita faruta, sai kurege kadima ya sake kashe ragowara dan nata ya lakwame. Domin kare laifin da ya aikata, sai ya karkarya rassan itatuwa yayi ta birgima a laka, yakuma shafa jar kasa a jikin sa kamar jini, yayi kamar anyi gumurzun fada.

Yayinda Nthoo ta komo gida, sai kurege yazo gare ta yana tafiya kata-kata yana kuka ya shaida mata cewar, wasu mutane ne suka zo suka kashe 'ya 'yan ta suka tafi dasu cikin kauye domin su cinye su. Yace yayi kokari domin kare 'ya 'yan amma maharbar suka nada masa dan karen duka, har ma sun kusa kashe shi. Shine ya nuna jar kasar da ya shafa a jikinn sa da cewa jinin dukan san ne.

Nan take Nthoo damisa tayi wani kugu cikin daren wanda ya girgiza jama'a. Cikin fushi ta nufi kauyen dake kusa dasu, domin daukar fansa kan mutanen da suka kashe 'ya 'yan ta. Yayinda damisa ke kokarin auka wa wasu yara sai taji wani tsuntsu yace Kadima ne ya kashe miki ya ya.

Sai Nthoo ta juya da baya a fusace domin aukawa Kadima kurege, amma yayinda Kadima yaji tautasuwar nan tana fadawa Nthoo sai yace kafa me naci ban baki ba. Nthoo damisa bata samu ta kama Kadima kurege ba, amma mutanenen Hambakush suce har yanzu Nthoo tana cigaba da neman Kadima. Shine yasa har yanzu damisa take kaffa-kaffa kana take farauta ita kadai. Kuma shi yasa kurege yake gudu a kodayaushe domin tsirar da ransa batare da yana waiwaye ba.

*When Hippo Was Hairy*

**Gibi Tsankanin maza da mata a makarantun Afrika 46secs**

Yara maza akafi dauka a makarantun Firamare da sakadare fiye da yara mata a akasarin kasashen Afrika. Gibin yakairabin yara mata ake dauka kan maza a kasashe 11 ciki harda Najeriya, da Ghana da Cote d'Ivoire, da jumhuriyar Benin da jumhuriyar denijyradiyar Congo. Wannan kuwa yana kunshe cikin sanarwar da majalisar dunkin duniya ta bayar.

Sama da kasashe 18 ne suke kokari wajen cike gibin, wadanda suka haka da Masar da Zimbabwe, da Uganda da Habasha da Cameru dakuma Algeria. Kasashe bakwai kuma basa nuna wannan bambancin, yayinda Afrika ta Kudu da Lesotho kuma yaran mata ne akafi dauka cikin makarantun fiye da yara maza.

*United Nations*

**Matsalar ingantacen ruwan sha 14secs**

Yanzu haka akwai kasashe 31 a duniya dake fuskantar matsalar karncin rwan sha. Yazuwa shekara ta 2025 ana kyautata Zato yawan kasashen zasu karu zuwa arba'in da tawas yazuwa shekara ta 2-50 kuma da zasuyi fama da matsakar karancin ruwan zasu kai 55.

*CGIAR*

**Italiya na daukar tsauraran matakai kan karya dokokin muhalli 44secs**

Yayinda take samun aiyukan cunna wuta a gandun dazuzzukan ta kowace rana yanzu kasar Italiya ta sanya tarar dala dubu 60 ga duk wanda aka kama da laifin cinna wuta a gandun dajin kasar. Kana za a bada kyautar wannan kudin ga duk wanda ya taimaka aka kamo wanda ya cinna wutar. Rahotanni sun nuna cewar masu cinna irin wannan wutar a Itlaiya suna janyo ta'adi mai yawa na katako da sauran gandun dazuzzukan kasar a duk shekara.

Kusan kowace rana sai an sami rahoton cinna wuta har sau 28 a locain bazara a shekaru biyar da suka wuce, yayinda filaye mai fadin kadada dubu dari biyar da arba'in ne suka kone, kamar yadda rahoton hukumar kula da halittu ta duniya tayi bayani.

*WWF*

**Bunkasar alkari'u cikin hanzari a Afrika 21secs**

Mutane sai kara baikin yankunan karkara suna zuwa birane a nahiyar Afrika fiye da kowace nahiya a duniya. Tsakanin shekarar 1995 zuwa 2025 yawan mutanen dake alkari'un Afrika zai rubanya har sau biyu a duniya, amma na Afrika zai rubanya sau uku a daidai wannan lokacin.

*Boiling Reint*

**Tsuntsun dake sanin locaci** **59secs**

Katabaji wani tsuntsu dake fadin locai? Wasu masu bincike kan halayyar tsuntsaye a kasar Indonesia sun gano wani abin sha'awa. Su wadan nan masu binciken da ake kira Pitta Erythro*gaster,* sun gano wasu tsutsaye masu launin ja a ciki suna iya sanin locacin dake ciki a duk twawon rana. Da asuba tsutsayen sukan sauka kasa su rika yin wata irin waka. Yayinda rana ta daga sai su hau kan bishiya har sai rana ta raba tsaka. Yayinda rana ta fara faduwa, sai tsutsayen su sauko daga rassan bishiyar har zuwa faduwar rana. Ba anan ta tsaya ba in har tsuntsayen sun sauka kasa batare da sun hau kan bishiya ba to ranan za'ayi ruwa.

*WWF*

**Asarar halittu** **34secs**

"Babbar asarar da zata auku ba wai rashin makamashi ba ko gurguncewar tattalin arziki, ko yaki da makaman kare dangi ko cinyewa da yaki ba. Duk da irin wadan nan ta'adi ko asarar, yan baya masu zuwa suna iya farfadowa dashi. Amma babbar asara itace wanda aka fara a shekarun 1980, wanda kuma zai dauki miliyoyi shekaru ba a gyara ba kamar yadda wasu halittun ke bata baki daya daga doron duniya. 'Yan baya masu zuwa bazasu gafarta mana ba muddin muka kauda wasu halittun batare da sun sansu ba.

*Edward O. Wilson*

**Kasar Canada na da nuhimmanci kan halittu** **26secs**

Canada keda kashi 10 cikin dari na dazuzzukan dake akwai a duniya, wanda yakai kadada milyan 418, wanda ya kai kimanin rabin fadin kasar baki daya. Wanan gandun dazuzzukan suan taimakawa wajen kula da kashi 20 cikin dari na ingantacen ruwan sha na duniya, wanda kuma nau'o'in dabbobi daban-daban har dibu dari da arba'in ne ke zaune a yanki. Bugu da kari kasar itace kan gaba wajen saida albarkatun dazuzzuka a duniya irin su katako.

*WWF*

# Kalmomin Da Akayi Amfanidasu

| | | |
|---|---|---|
| AAI | - | Kungiyar kawance bunkasa masana'an ta Afrika |
| ADB | - | Bankin raya Afrika |
| AIDS | - | Cutar Kanjamau |
| CGIAR | - | Kungiyar kwararu kan binciken aikin gona |
| ECA | - | Hukumar raya tattalin arziki na Afrika |
| FAO | - | Hukumar abinci da aikin gona ta duniya |
| HIV | - | Kwayoyin cutar kanjamau |
| NCF | - | Hukumar kula da gandun daji ta Najeriya |
| NGO | - | Kungiyoyi masu zaman kansu |
| OAU | - | Kungiyar hada kan kasashen Afrika |
| UN | - | Majalisar Dukin duniya |
| UNDP | - | Hukumar raya kasa ta duniya |
| UNIDO | - | Hukumar raya masana'antu ta duniya |
| UNITA | - | Kungiyar 'yan tawayen Angola |
| WWF | - | Asunsun kula da gandun daji da halittu |